Labaru

Offishin Jakadancin Amirka, Sashen Hulɗa da Jama'a,
Plot 1075 Diplomatic Drive, Central Business District, Abuja.
Telephone: 09-461-4000. Website at *http://nigeria.usembassy.gov*

# Jawabin Ambasada John Campbell, Jakadan Amirka a Nijeriya a Wajen Bikin Tunawa da Harin 11 ga Watan Satumba da Akayi a Cibiyar 'Yan Jaridu na Kasa a Abuja

Yau a garin Abuja mun shiga sahun sauran abokai da 'yan uwa a duniya baki ɗaya wajen yin juyayi da kuma tuna hare-haren ta'addanci da aka kai garurruwan New York da Washington, a ranar 11 ga watan Satumba, watau shekaru biyar da suka gabata. Wannan ranar juyayi da kuma sauran ranaku irinta ba batu bane na Amirka, ko Amirkawa, kawai, batu ne wanda ya shafi kowa da kowa.

Wannan ranar juyayi tana tunatar da ɗaukacin al'umman duniya ba tare da banbancin jinsi ba, babban nauyi da ke kan mu na tinkaran waɗanda ke yaɗa akidar tsana da kashe-kashen rayuka da lalata dukiyoyi ba gaira ba dalili. Bayan haka ma, ranar ta bamu dama domin sake jaddada matsayin mu na yin Allah wadai da duk ayyukan ta'addanci.

Wadanda hare-haren 11 ga Satumba ya ritsa da su, mutane ne daga ƙasashe daban-daban sama da 90, kuma mabiya addinai ne dabam-dabam da suka haɗa da addinin Kirista, da addini Yahudu da kuma addinin Musulunci.

Wannan banbanci na addinai tsakanin waɗanda suka rasa rayukan su a harin 11 ga watan Satumba na nuna mana cewa babu wani addini daya amince da duk wani aiki na ta'addanci, kamar kisan kai ko kuma sacewa da kuma yin garkuwa da mutanenda bas u san hawa ba, basu san sauka ba.

Haka kuma wannan rana ta yau na tunatar da mu irin bala'i da baƙin ciki da ayyukan ta'addanci suka jawo wa jama'a da dama a ƙas ashen duniya masu yawa, musanman a Indonesiya da Moroko da Spain ko Andalus da Jordan da Ingila da Indiya da Tarayyar Kasar Rasha da kuma Masar.

Babban burin 'yan ta'adda shine su tilastawa sauran mutane akidar su ta ƙiyayya da rashin haƙurcewa juna kan banbancin salo ko na fahinta. Ta irin ayyukansu na kashe-kashen rayuka, 'yan ta'adda na nuna akidar su na rashin girmama rai, wanda kuma yake nuna rashin girmama Ubangiji da halittun Sa.

Yaƙin da duniya keyi da ayyukan ta'addaci yana nuna irin yadda baki ya zo ɗaya kan manyan muradun duniya; duk bil-adama yana sha'awa kuma ya na da 'yancin faɗin

albarkacin baki da ’yan cin addini daya ke so da kuma yin walwala ba tare da wata tsangwama ba.   Haka nan kuma duk addinan duniya sunyi umarni da yin adalci da nuna tausayawa ga mabukata da nuna soyayya ga iyali da girmama al’ummar da muka fito cikinta.

Kodayake ƙungiyar Al-Ka’ida na ƙokarin nuna cewa duniya  na tsakiyar gwagwarmayar samun ikon faɗa aji ne tsakanin muradu da akidu dabam-dabam, gaskiyar maganar itace, a faɗin duniya baki ɗaya ana ƙara samun haɗin kai wajen fuskantar manyan matsaloli na yau da kullum tare da samara da tallafi ga al’umominda ke bukatan agaji.

Muna jinjinawa hukumomin birnin Landan saboda irin bajintar da suka nuna wajen daƙele gagarumin shirin aikata ta’addanci wanda da zai kai ga halaka jama’a ba tare da hakkinsu ba.  A yanzu muna cigaba da samun haɗin kai daga ƙas ashen duniya domin samar da yanayin zaman lafiya mai ɗaurewa da rayuwa mai inganci a duniya baki ɗaya.

A wannan rana na tunawa da kuma juyayi domin girmama rayukan waɗanda harin 11 ga watan Satumba ya ritsa da su, mu Amirkawa na jaddada manufofin magabatan mu, na cewa duk bil-adama daidai suke a gaban Ubangiji, don haka tilas ne ko wani mutum ya zauna cikin ’yanci, walwala da adalci.  Na gode.